



# KASUWANCIN KU GOBEN KU

**Ainhin Jagora Kaddamar da Kasuwanci wa Baƙi Ƴan kasuwa**



# Godiya

**Kungiyar Shige da Fice ta New York da Cibiyar Ci gaban Al'umma ta Pratt ne suka kirkiri wannan jagoran, a matsayin wani yunƙuri na ƙara samun cikakkun bayanai da abubuwa ga baƙi yan kasuwa a New York. An sami kuɗaɗen da aka wallafa wannan jagoran daga Capital One, Ma'aikatar Matasa da Ci gaban Al'umma ta NYC, Majalisar Birnin New York da Ofishin Kakakin Majalisa, ta hanyar kungiyar Haɗin Kan Shige da Fice na New York zuwa Kaddamarwar Birni.**


An buga a watan Afrilu na 2019

Ben Dodd ne ya tsara, da gudunmawa daga Sydney Céspedes, Sal Muñoz

Misalai daga June Lee


## Kungiyar Shige da Fice ta New York

Kungiyar Shige da Fice ta New York ƙungiya ce mai zaman kanta wacce ke hasashen Jihar New York wacce take da ƙarfi saboda jama'a sunyi maraba da ita, suna yin adalci akan kowa sannan kuma an basu damar cimma burin su. Kungiyar haɗin kan baƙi, mabiya da abokan tarayya da yadda duk mazauna New York zasu bunkasa

## Cibiyar Pratt don cigaban al'umma

Cibiyar Pratt don cigaban al'umma sun haɗa da tsara birane, bincike, bayar da shawarwarin siyasa, da taimakon ƙananun kasuwanci don baiwa al'ummomi masu karamin karfi da matsakaicin karfi don tsarawa da kuma gane makomarsu don samun daidaito da ingantaccen birni mai dorewa ga duk mazauna New York.

# TEBURIN ABUBUWAN DA SUKE CIKIN NAN


Fara Kasuwancin? Abun da ya kamata Ku sani! ........ 6

Yadda za ku yi amfani da wannan jagoran ........ 6

Farawa ........ 7

Nasihu don Zaɓin Tsarin Kasuwanci ........ 11

Tsarin kasuwanci guda 6 ........ 15

Mallakar kai ka dai ........ 16

Haɗin gwiwa na Gaba Ɗaya ........ 17

Haɗin gwiwa Mai Iyaka ........ 19

Kamfanin Lamuni Mai Iyaka (LLC) ........ 21

Kamfani ........ 23

Haɗin gwiwar Ma'aikata ........ 26

Ma'anoni ........ 27

Muhimminan Takardu ........ 28

Albarkatu ........ 29

# Saƙo daga Kakakin Majalisar Birnin New York Corey Johnson


Ya ku mazauna New York,

Birnin New York da muka sani da kuma mu ke ƙauna ba zai zama kome ba in babu baƙi yan kasuwa. Baƙi su ne ƙashin bayan tattalin arzikin yankin mu, tare da yawan ma'aikatan da kuma mallakan kasuwanci. A ƙashin gaskiya, baƙi sune suka mallaki rabin kasuwancin birnin New York sannan sun ba da gudummawar dala biliyan 228 ga GDP na Birni a shekarar 2017. Duk da haka, akwai wasu albarkatun musamman da aka tanada don taimaka wa masu kasuwanci na baƙin. Na yi farin cikin ƙara wannan albarkatu a cikin akwatin kayan aiki na ƙoƙarin Birnin wajen tallafawa don bunƙasa ɓangaren kasuwanci mallakar baƙi. Wanan hanya ne mai inganci wajen tabbatar da cigaba da cire shingen da ke kare cigaba wa duk mazauna New York.

A daidai lokacin da baƙin New York masu aiki tukuru ke fuskantar farmaki daga gwamnatin tarayya, ina alfahari da cewa majalisar gari ta goyi bayan ƙirƙirar wannan jagorar. "Kasuwancin Ku Goben Ku" ita ce cikakken tattaunawa mai yawa da masana shari'a akan shige da fice, kasuwanci, da kuma haraji, da kuma ƙungiyoyin baƙi da yan kasuwa. A hanyoyin da yawa, shine na farko a irinsu. Wannan jagoran ya bada hanya ɗodar da kuma bayanai mai amfani ga duk baƙin New York masu sha'awar fara kasuwanci amma basu san wane hanya za su ɗauka a gaba ba ko kuma ba su san ma wannan irin kasuwancin za su buɗe ba.

Ba wai kawai wanan jagoran abun mai matukar muhimmanci ga yan New York ba, amma buga shi a wannan lokaci ya tura saƙo mai karfi daga majalisan akan baƙin New York ana maraba da su anan da kuma muna daraja yawancin gudunmawar da kuke bawa Birnin. Fatana ne wannan jagorar ta zaburar da duk mazauna New York don ɗaukar wannan mataki na gaba!

Cikin hidima,



Shugaban Majalisar Birnin New York

Corey Johnson

# Saƙo daga Manyan Daraktoci


Sama da shekaru 150, New York ya kasance tushen dammammaki ga baƙi. Sannan kuma su kuma suna ci gaba da karfafa tattalin arzikin ta. Baƙi sun ƙunshi kashi ɗaya bisa huɗu na ma'aikatan New York kuma suna ba da gudummawar biliyoyin daloli kuɗaɗen shiga wa jahar. Amma ba wai kawai baƙin suna ƙara gyara ma'aikatan New York ba ne, suna tsara shi sosai: Sama da yan kasuwa 83,000 a birnin New York baƙi ne, su suka haɗa mafi yawan ma mallakan ƙananun kasuwanci.

Kungiyar Shige da Fice ta New York da Cibiyar Pratt don Ci gaban Al'umma suna alfahari da samar da wannan jagorar a matsayin hanya mai sauƙi don taimakawa baƙi farawa da ci gaba da cin nasara a kasuwanci. Akwai ɗimbin hanyar sadarwa na ƙungiyoyin jama'a, incubators, ƙananun ayyukan kasuwanci, da masu ba da doka waɗanda ke ba da ayyuka masu mahimmanci ga yan kasuwa, amma da yawasu, abubuwan da akayi amfani dashi ba su iya yaren ba. Wannan matsala ne ga duk yan kasuwa amma musamman ga baƙi idan aka yi la'akari da matsalolin rashin iya yaren da al'adu da suke fuskanta.

Wannan jagoran ya fara da magance wasu daga cikin sanannun matsalolin da baƙi ke fuskanta ta hanyar samar da bayanai da yarurruka daban-daban. Wannan hanyar ilimi za ta taimaka wa abokan hulɗar al'umma waɗanda ke aiki a ƙasa don bada shawararin kasuwanci mai mahimmanci ga al'ummomi baƙi. Tallafawa kasuwancin baƙi da ayyukan da suke ƙirƙira yana da mahimmanci ga ci gaban tattalin arzikin New York gabaɗaya sannan kuma zai haifar da ƙarin dama ga duk mazauna New York.

Da gaskiya





Stave Choi
Darekta zartarwa
Kungiyar Shige da Fice ta New York

Adam Friedman
Darekta zartarwa
Cibiyar Pratt don Ci gaban Al'umma

# FARA KASUWANCIN?
# ABUN DA YA KAMATA KU SANI!

## Yadda za ku yi amfani da wannan jagoran

Kasuwancin baƙi shi ne kashin bayan tattalin arzikin kasar nan. A jahar New York, Baƙi ma mallaka kasuwanci sun kai kashi 33.8% na duk mallakan kasuwancin mallaka ƙashin kai na mazaunan, wanna suke samar da sama salla biliyan 7.2 na kuɗin shiga.[1] Yayin da baƙin adadin su ya ninki kashe biyu na yan asalin Amurka don fara kasuwanci, akwai abubuwan da aka keɓe musamman don taimaka wa baƙi ma mallakan kasuwanci.[2]

**An ƙirƙiri wannan jagorar don duk baƙi masu fara kasuwanci da kuma yan kasuwa, ba tare da la'akari da matsayin na baƙi ba, don taimaka muku fahimtar zaɓuɓɓukanku da kuma fara gudanar da kasuwancin ku a jihar New York.** Ansamar da wannan jagoran akan ayi duba ga bayyanai wanda ya haɗa da bayanai don taimaka muku wajen yanke shawarar akan wane nau'in tsarin kasuwanci ne ya dace da ku, menene buƙatun da ake bukata don kafa kasuwancin ku da wasu kudade da haraji da kuke tsammani domin cigaban kasuwancin ku.

Wannan jagorar baya ɗauke muku buƙatu cika sharruɗonɗin kamar su lasisi ko izini wanda za a iya buƙatar su a wasu masana'antu ko ma'aikatu. **Wannan jagoran ba shawarar doka ko haraji ya ke samar muku ba.** Baƙi yan kasuwa ana so sune mi shawarwarin masana doka dangane da shige da ficen ku, kasuwanci, ko sharruɗonɗin haraji da kuma abubuwan da a ka hane ku. Don ƙarin bayani, ku tuntuɓi sashin abubuwan wannan jagoran. Bayanan da ke cikin wannan jagoran ya kasance sabo a wannan wata na Oktoba na shekara 2018 kuma ba za a sabunta su ba.

1. "Baki a New York." (4 ga watan Oktoba na shekara 2018) Majalisar shige da fice ta Amurka. www.americanimmigrationcouncil.org/research/immigrants-in-new-york
2. "Batun Tattalin Arziki don Marabtan Baki Yan Kasuwa." (8 ga watan Satumba na shekara 2015) gidauniyar Kauffman. www.kauffman.org/what-we-do/resources/entrepreneurship-policy-digest/the-economic-case-for-welcoming-immigrant-entrepreneurs

# Farawa

## Tsakanin Dan kwangila mai zaman kansa da Ma'aikaci? (sannan kuma me yasa yake da mahimmanci)

Yawancin baƙi na fuskantar tarnaki wajen neman aikin da ake biyan da kyau sosai a Amurka. Mallakar kasuwanci na iya baiwa baƙi damar ci gaba ta fuskar tattalin arziki. Musamman, idan ba ku da izinin yin aiki a Amurka a matsayin ma'aikaci, fara kasuwanci ku zai taimaka mu wajen abun da za ku riƙe kan ku.

Harmun ne ga masu ɗaukan ma'aikaci su ɗauki wani da suka sani ba a basu izinin aiki a Amurka. Duk mai ɗaukan ma'aikaci yana da bukatar ya bincika ma'aikaci yana da izinin aiki ta:

- Cika wannan takardar I-9
- nazarin takardun shaida na ma'aikaci (kamar su lambar zamantakewa, kore katin, fasfo da sauran su)

Babu takamaiman dokar tarayya ko jihar New York da ta hana baƙi da ba su da izinin aiki mallakar kasuwanci, ko daga zama dan kasuwa mai cin gashin kansa. Dan kasuwa mai cin gashin kansa wani lokacin a na kiran sa da "dan kwangila mai zaman kansa." Dan kwangila mai zaman kansu ba kowane lokaci bane a ke sai sun cika takardan I-9 ga abokan cinikayya su lokacin da suka fara sabon kwangila. Idan ku ka kirkiri kasuwanci a matsayin na daban a matsayin doka kamar yadda aka bayyana a wannan jagoran, shima zai iya yin kasuwanci na kansa, wanda ciki har da samar da kayayyaki da ayyuka da kuma shiga kwangila.

A matsayin zahirin al'amari mai amfani, mafi yawan baki na iya samun abu yi ta hanyar fara kasuwanci ba tare da la'akari da matsayinsu na baƙi ba. Yana da muhimmanci a matsayin ku na yan kasuwa, kun bi dokokin da suka shafi gudanar da kasuwancin ku, gami da biyan haraji. Ya kamata ku fahimci cewa fara kasuwanci yana buƙatar gabatar da takardu ga hukumomin gwamnati da bankuna, baya hana a kore ku daga Amurka sannan kuma bai baka kariya daga doka ba. Duk da haka, a wasu lokuta, alkalai a cikin shari'ar shige da fice na iya bada fili kan mallakar kasuwanci da biyan haraji.

## Yadda za a gane idan ku yan kwangila ne masu zaman kansu

Yana da ma matukar wahala a iya ganewa shine ku yan kwangila ne ko ma'aikata ne sannan kuma ya kamata ku nemi shawarar doka koyaushe dangane da takamaiman yanayin ku.

Yan kwangila masu zaman kansu suna shiga kasuwanci don kansu ne kawai da kuma suna samar da kaya ko ayyuka ga abokan cinikayya su. Akasarin ku, da abokan cinikayya ku, kuna sarrafa yadda kuke samar da kaya ko ayyuka da fannin da ya shafi kuɗaɗen kasuwancin ku, mafi kusantar cewa za a ɗauke ku a matsayin ɗan kwangila mai zaman kansa ba ma'aikacin abokin cinikin ku ba. A shafi na gaba za ku samu misali a cikin jerin sunayen na da yake kwatanta matsayin ma'aikaci da dan kwangila mai zaman kansa.


Idan kuka kafa wata doka don kasuwancin ku, ita dokan da kanta zata iya samar muku da kaya da kuma ayyuka ga abokan cinikayya ku. A gaba ɗaya, Wataƙila ba za a ɗauke ku a matsayin ma'aikaci ba **indan duk kan ku mallaki kuma ku na sarrafa kasuwancin ku.** Don wannan dalili, ana ba da shawarar cewa yan kasuwa waɗanda ba su da izinin aiki:

- mallaki duka ko wani muhimmin sashi na kasuwancin ku, da
- sarrafa ayyukan kasuwancin ku.

# Ma’aikata ko Yan kwangila Masu zaman kansu?

Ina aiki a matsayin mai kula da gida kuma ina samar da ayyukan na ga abokan hulɗan da yawa. Ina da gidan yanar gizon da ke bayyana farashin ayyukan da nake samarwa. Ana biya na akan ayyukan na, ba albashin sa’a-sa’a ba. Abokan hulɗanna na iya neman na ta yin alƙawari dani ta yanar gizo ko ta wayana. Abokan hulɗanna suna samar da nasu kayan tsaftacewa da kayan aiki su.

Ina aiki a matsayin mai kula da gida ma wasu iyali daga Litinin zuwa Juma’a daga 8 na safe zuwa 4 na yamma. Mun daidaita da su akan dala 15 a kowane sa’a sanan kuma mun daidaita zai dinga ƙaruwa duk shekara don magance al’amurra yau da kullum. Iyalan da na ke aiki dasu su suke samar da kayayyakin tsaftace da aikace-aikace. Su kan bar mu rubuttacen umarni akan abun da ya kamata in yi a kowane rana. A ƙarshen mako na kan yi ma da wasu iyalan don samun ƙarin wasu kuɗin.



| | Mai Kula da gida A | Mai Kula da gida B |
|---|---|---|
| Ajiye wurin kasuwanci | | ✓ |
| Muhimmin saka jari a kan kayan aikin ku, abubuwan, kayayyaki, kayayyakin aiki da kuma abubuwa | | |
| Ɗaukar alhakin hadarin kudi don riba ko asara | | ✓ |
| Tsara ko daidaita ƙimanta kuɗin da za a biya ku | ✓ | ✓ |
| Za ku iya zabar naku mai taimakon | | ✓ |
| Kuna da ‘yanci don ƙin tayin aiki | | ✓ |
| Za ku iya samar da ayyuka ma abokin hulɗan ku | ✓ | ✓ |
| Sarrafa yadda, lokacin da kuma inda ake yin aikin | | ✓ |
| | NI MA’AIKACI ne | Ni DAN KWANGILA MAI ZAMAN KANSA |

# Ma'aikaci ko Dan kwangila mai zaman kansa?

Ni akawun kamfani ne in suna da buƙatar aiki na, idan kamfani na bukata na za su tattance wane kwanaki zan musu aiki da kuma tsayon wane lokaci. Ana biya na indan na kammala aikin sannan kuma ba albashi sa'a-sa'a ake biyan na ba. Lokacin da nake bukatar a biya ni na kan aika wa kamfani daftari. Nayi aiki wa wasu kamfanoni masu yawa wanda aiki akawon su sunyi kama da juna. Ina aiki daga ofishinna na gida sannan kuma nayi amfani da kwamfuta aiki na.

Ina aikin minti 30 a sati, na dan lokaci a kamfani a matsayin akawun sannan a biya ni albashi sati-sati. Akasarin adaga gida da kuma na kayi amfani da kwamfuta na. In naso, , Zan iya yin rajista don cin ribar fa'idodin kiwon lafiya tare da kamfanin da nake aiki da shi. Wani lokaci akan karbi aikin daga wasu kananun kamfanonin a lokacin da ba na aikin wancan Kamfanin.





| | Akawun A | Akawun B |
|---|---|---|
| Ajiye wurin kasuwanci | ✓ | ✓ |
| Muhimmin saka jari a kan kayan aikin ku, abubuwan, kayayyaki, kayayyakin aiki da kuma abubuwa | ✓ | ✓ |
| Ɗaukar alhakin hadarin kudi don riba ko asara | | ✓ |
| Tsara ko daidaita ƙimanta kuɗin da za a biya ku | | ✓ |
| Za ku iya zabar naku mai taimakon | | ✓ |
| Kuna da 'yanci don ƙin tayin aiki | | ✓ |
| Za ku iya samar da ayyuka ma abokina hulɗan ku | ✓ | ✓ |
| Sarrafa yadda, lokacin da kuma inda ake yin aikin | | |
| | Ni MA'AIKACI NE | Ni DAN KWANGILA MAI ZAMAN KANSA |

# Nasihu don Zaɓin Tsarin Kasuwanci

Yanzu da ku ka yanke shawarar fara kasuwanci, kuna buƙata gano wane irin kasuwanci ne ya dace da ku! Wanna shashen ya samar da bayanai akan zaɓi daban-daban da ku ke da shi na tsarin kasuwanci.

Wasu tsarin kasuwanci suna da ƙayyadaddun dokoki masu tsauri da tsadar kuɗin fatawa. Wasu kasuwanci suna da sauƙin buɗewa, da kaɗan zuwa babu buƙatar aikin takardu, ko kashe kuɗin kaɗan, amma mai kasuwancin yana da haɗarin kuɗi mafi girma. A maimakon ku zaɓi tsarin kasuwanci mafi dacewa da buƙatun ku, yana da mahimmanci ku fahimci wasu mahimman ra'ayoyi game da nau'ikan kasuwanci a cikin Jihar New York.

## Kare Kuɗaɗen ku

Kasuwanci na iya zama mahallin doka wanda ke bambanta da mai kasuwanci. Shi Kungiyar doka kamar mutum yake, tana da ikon doka wajen shiga yarjejeniya ko kwangila, tana ina iya karba bashi da kuma ta kan iya ba da bashi, tana ina iya kai kara da kuma akan kai ta kara sannan ta kan dauki alhakin ayyukanta.

Lokacin da kasuwancin ku keɓaɓɓen mahaɗan doka ne za ku iya samun **lamuni na sirri mai iyaka.** Alhakin ku na basussukan kasuwancin gabaɗaya ya ta'allaka ne da jarin ku a cikin kasuwancin. Idan kasuwanci ku daban yake da sauran kasuwanci ku sannan za a iya kai ta kotu, kadarorinku kamar gidank ko motarku, gabaɗaya suna cikin aminci daga kwace su saboda a maye gurbin da'awar da akayi akan kasuwancin. Wani fa'idar gudanar da kasuwanci ta hanyar wata ƙungiya ta doka ita ce ƙungiyar da kanta na iya yin kasuwanci bisa doka ko da mai shi ba shi da izinin yin aiki ko yana gudanar da kasuwancin daga wajen Amurka.

A wannan jagoran, mun tattara farashi da fa'idodin wanda nau'ikan ƙungiyoyin doka waɗanda za a iya kafa su a cikin Jihar New York don lamuni na sirri mai iyaka: Haɗin gwiwan Mai Iyaka, Kamfanin Lamuni Mai Iyaka, da kuma kamfani.

Don fa'ida daga keɓaɓɓen **Lamuni Mai Iyaka** na ƙungiyoyin doka don kasuwancin ku:


- tabbatar da kun ware keɓaɓɓen kadarorin ku daga kadarorin kasuwancin ku
- bude asusun banki na daban don mahaɗin ku na doka
- yi amfani da sunan ƙungiyar doka a wajen kwangila da kuma tallace-tallacen ku ( a maimakon sunan ku)
- Karbi lambar haraji ID (EIN) na daban da kuma shigar da bayanan harajin daban don mahaɗin ku na doka wajen da lokacin da ake buƙata.

## Menene ITIN?

Lokacin da ka samu kuɗin shiga ya zama wajibi ka biya haraji. Lambar Shaida ta Mai Biyan Haraji (ITIN) masu hada-haɗan Harajin Cikin Gida (IRS) ne ke bayarwa ga mutanen da ba su cancanci karɓar lambar tsaro ba amma dole ne su shigar da haraji. Idan kuna da lambar tsaro (SSN) ba ku cancanci lambar ITIN ba. Ko da izinin aikin ku ya ƙare, SSN ɗinku ko yaushe yana kasancewa mai inganci don dalilin shigar da haraji. Haka nan zaku iya amfani da ITIN don karbar ayyukan kuɗi masu yawa wada suka haɗa da samun damar karbar bashi ko buɗe asusun banki, ba tare da la'akari da matsayin ku na shige da fice ba. Don ƙarin bayani ku duba Kuɗin ku gobenku Babban Jagora don Ilimin Kuɗi da Karfafawa, hanya don taimaka wa baƙi su fahimci zabuɓɓukan kuɗi na sirri.

## Menene EIN?

Don dalilai haraji na tarayya da na Jihar New York, duk kasuwanci da yake da ma'aikata dole ya karbi Lam-bar Shaidan Ma'aikata (EIN). Kamfani da Kamfanonin Lamuni Mai Iyaka (LLCs) dole ku mallaki EIN. Yawanci, Bankuna na buƙatar EIN don buɗe muku asusun kasuwanci ku na banki. Don samun EIN, kasuwanci zai na iya tura takardan SS-4 ("Aikace-aikacen Lambar Shaida ta Ma'aikata") zuwa ga IRS ko ku cika ta waya ko a yanar gizo.




## Fahimtar Wajiban Haraji na Kasuwancin ku

Ba tare da la'akari da matsayin ku na shige da fice ba, kowane mai samun kuɗin shiga a Amurka dole ya biya ga gwamnatin tarayya, jiha da kuma kananan hukumomi. Bukatun haraji sun dogara da abubuwa da yawa wadan sun haɗa da ko kun yin rajista a matsayin marar aure ko kuma mai aure, kuɗi da ku ka samu a shekara, sannan kuma da ina ku ke zauna a cikin New York.


Gabaɗaya, mafi sauƙi tsarin kasuwancin ku shine mafi sauƙin bukatun harajin ku na kan iya zama. Akwai wasu tsarin kasuwanci da ya ba ku dama ku bada rahoton kuɗin Shigan da ku ka samu daga kasuwancin ku akan harajin ku na kan kanku, wanda zai iya sauƙaƙe shirye-shiryen haraji ga masu kasuwanci.

**Dan Allah ku sani wannan jagoran ba manufarsa baku shawarar haraji ba. Ana ƙarfafa yan kasuwa baƙi su nemi shawarar haraji daga ƙwararrun masana haraji.** Sashen albarkatun kuma yana yin nuni ga ƙungiyoyi waɗanda ƙila su cancanci su taimaka muku da tambayoyin haraji game da kasuwancin ku.

# Labarin Kasuwanci Guda Biyu

## Kamfani Lamuni Mai Iyaka*

Abokai uku suka fara kasuwanci gyara shimfidar filaye tare. Suka yi rigistan kasuwancn a matsayin Kamfanin Lamuni Mai Iyaka (LLC). Shi LLC ɗin su wani yanki ne na doka daban.





Kowane mamba ya saka jarin dala 400 don kuɗin farawa sannan kuma kamfanin ya karbi **bashin kasuwanci** daga banki.

Kasuwancin bai ci nasara ba sannan kuma a ka kulle shi bayan yan wasu watanni da kuma bashi da a ke bin kamfani dala 8000.




Wannan asarar ta tsaya akan iya dala 400 da kowane mamba na kamfanin lamuni mia iyaka ya bayar ne da da kuma sauran kadarorin kamfani.





Ma mallaka kamfani basu da damuwa da bashin LLC ba sannan kuma kadarorin su sun tsira.



## Mallakar kai ka dai

Me mallakar kai ka dai ta fara kasuwanci gyaran shimfida filaye. Ita da kasuwancin ta ana mata ganin abu ɗaya na a karƙashin doka.




Ta saka jarin dala 400 na ajiyar ta sannan kuma ta **karɓe** katin bashin don sayi kayayyakin aiki ma sabon kasuwancin ta

Kasuwancin bai ci nasara ba sannan kuma an kule da bashin dala 8000 a katin bashii dala 8000




Tayi asarar dala 400 da ta saka jarin sannan kuma yanzu alhakin bayin dala 8000 na katin bashi yana kan ta tare da kuɗin ruwa.




Idan bata biyan kuɗin ba, kamfanin katin bashin za su zo su kwace kadarorin don su biya bashin wanda ya haɗa da mota, gida, da kuma ajiyar ta!



*Anyi nuni da LLC a cikin wannan misalin, amma sauran nau'ikan ƙungiyoyin doka da aka tattauna a baya a cikin wannan jagorar suma suna iyakance alhaki yana kan mutum.

# TSARIN KASUWANCIN IRI DAYA GUDA 6

Akwai kala kala kasuwanci iri daya guda shida a jahar New York da alaƙa da baƙin yan kasuwa. Sun haɗa da jerin wannan:

- **Mallakar kai ka dai**
- **Haɗin gwiwa na Gaba Ɗaya**
- **Haɗin gwiwan Mai Iyaka**
- **Kamfani Laumuni Mai Iyaka (LLC)**
- **Kamfani**
- **Haɗin gwiwar Ma'aikata**

Wannan jagoran ya samar da bayanai akan tsarin kasuwanci guda biyar ɗin farko ne. Ana iya kafa karkashin haɗin gwiwa ta hanyar haɗin gwiwa, LLCs, ko kamfani. Saboda tsarinsa na musamman. Wannan jagorar baya ba da cikakken bayani a kan buƙatun kasuwanci da wajibai na haɗin gwiwa. Don ƙarin bayani akan kamfani hadin gwiwa, duba shashin albarkatu.

# Mallakar kai ka dai

Mallakar kai ka dai shine tsarin kasuwanci mafi sauƙi da za kayi amfani da shi wajen hulɗan kasuwancida kuma mafi sauƙi haɗawa, Wataƙila ka riga ka zama mai mallakar kaɗaici idan ka samar da ayyuka ko sayar da kaya ko da ba tare da shigar da kowane takarda tare da gwamnati ba. Kuɗin farawa kadan ne saboda baka buƙatan ka biya wani kuɗi ko ka ba da wani takardu kamar yadda ake buƙata a sauran tsarin kasuwanci. Za ka ba da rahoton samun kuɗin Shigan kasuwanci ne a harajin ku na kan kanku, don haka shirye-shiryen haraji yana da sauƙi.

| Takaitacciyar Jawabin Mallakar Kai ka dai | | |
|---|---|---|
| # na masu shi | **1 Maishi** | Mutum ne kawai mai kasuwanci |
| Farawa | **Sauƙin farawa** | Yana haduwa ne da zaran kun fara gudanar da ayyukan kasuwancin |
| Kuɗi/Takardun | **Babu ko kaɗan** | *(Na zaɓi)* Kudin shigar da ƙara na yau da kullun, wanda ya bambanta daga gundumomi, don Takaddun Sunan da ku ka Sa idan sunan kasuwancin ya bambanta da na ku. |
| Shirin Haraji | **Mafi sauƙi** | Za Ku bayar da rahoton samun kuɗin shiga na kasuwanci ku bayanin ku na kuɗin shiga na harajin na kan kanku. |
| Lamuni | **Mai girma haɗarin kuɗi na kan kin kai** | Mai kasuwanci shi ke da alhakin duk basussuka da wajibai na kasuwancin, sannan kuma kadarorin mutum na cikin haɗari |
| Abubuwan da a ke da buƙata masu gudana | **Babu sabuntawa mai gudana/filings** | Bai zama wajibi ba akan sai ka kaddamar da wani ƙarin ƙararraki ga kowace hukumomin gwamnati don kula da mallakar kai ka dai. |
| Da kyau Don | Aikin gyaran wutan lantarki, masu shimfidar wurare, masu aikin gida, mai koyarwa, masu rubutu, da kuma masu fasaha | |

# Haɗin Gwiwa Na Gaba Ɗaya

Haɗin gwiwa na gaba ɗaya ya kan yi aikin sosai wa ma mallaka kasuwanci biyu ko uku wadan da su ke neman su raba hadari kuɗi da kuma yanke shawarar tare. Wannan yana aiki ne wa ma mallaka kasuwancin da su ka yarda da juna saboda kowannen su yana da alhakin wajen yake shawarar dan uwansa.

Kamar mallakar kai ka dai, akwai kaɗan ko ma babu bukata takardun wajen kirkiran Haɗin gwiwan Gama gari. Wataƙila kun riga kun kasance cikin haɗin gwiwa na gaba ɗaya idan kun tsunduma cikin ayyukan kasuwanci tare da wani mutum kuma kun riƙe kanku a matsayin abokan hulɗa a kasuwanci. Ana ba ku shawarar cewa ya kamata da ku da abokan haɗin gwiwa ku samar da yarjejeniyar haɗin gwiwa, takarda mai mahimmanci wanda ke bayyana menene haƙƙin kowane abokin haɗin gwiwa, nawa kowane abokin haɗin gwiwa ke saka hannun jari, da kuma yadda abokan haɗin gwiwa ke magance matsaloli. Sai dai idan akwai wata yarjejeniyar haɗin gwiwa da ta bayyana akasin haka, duk riba da asarar za a raba shi daidai tsakanin abokan haɗin gwiwa. **Ya kamata ku nemi taimakon masana doka wajen haɓaka yarjejeniyar haɗin gwiwa.**

Kamar yadda yake da mallakar kai ka dai, ba a kare kadarorin ku ba a wannan tsarin haɗin gwiwa na gaba ɗaya, kuma kadarorin keɓaɓɓen abokin tarayya na iya zama cikin haɗari sakamakon rashin yanke shawara na abokin haɗin gwiwa.

## Yarjejeniyar Haɗin gwiwa

Yarjejeniyar haɗin gwiwa wata muhimmiyar takarda ce da ke bayyana haƙƙoƙin kowane abokin haɗin gwiwa ke da shi game da kasuwanci. Yarjejeniyar haɗin gwiwa ana matuƙar ba da shawarar ga abokan haɗin gwiwa na gabaɗaya da su yi shi don ƙakkarfan haɗin gwiwa. Yarjejeniyar haɗin gwiwa tana amsa wadan nan tambayoyin masu zuwa:

- Nawa kowane abokin haɗin gwiwa zai saka jari?
- Menene ayyukan kowane abokin haɗin gwiwa?
- Ta yaya abokin haɗin gwiwa zai yake shawara?
- Ta yaya abokan haɗin gwiwa za su raba roba da kuma faɗuwa?
- Ta yaya abokan haɗin gwiwa za su raba rikici a tsakanin su?
- Me zai faru in abokin haɗin gwiwa yace zai bar kasuwanci ko sayarwan nashi ribar kasuwanci?

## Takaitacciyar jawabin Haɗin gwiwar Gabaɗaya

| | | |
|---|---|---|
| # na masu shi | **Masu shi 2+** | Abokan haɗin gwiwa ne suka mallaki kasuwancin. |
| Farawa | **Sauƙin farawa** | Ta na kafuwa da zarar kun gudanar da ayyukan kasuwanci. |
| Kuɗi/Takardun | **Babu ko kaɗan** | *(Na zaɓi)* Kudin shigar da ƙara na yau da kullun, wanda ya bambanta daga gundumomi, don Takaddun Sunan da ku ka Sa idan sunan kasuwancin ya bambanta da na ku. Ana ba ku shawarar yarjejeniyar haɗin gwiwa. |
| Shirin Haraji | **Sauƙi** | Abokan haɗin gwiwa su kan ba da rahoton samun kuɗin kasuwanci a rahoton harajin su ne. Hakanan ya kamata a shigar da bayanan haɗin gwiwa. |
| Lamuni | **Mai girma haɗarin kuɗi na kan kin ka** | Kowane abokin haɗin gwiwa za a iya samun shi da alhakin akan abin da a abokin haɗin gwiwar sa ya aikata. Kadarorin ku na kashin kan ku na ciki haɗari. |
| Abubuwan da a ke da bukata masu gudana | **Babu sabuntawa mai gudana/filings** | Ba ku da buƙatan da ku gabatar da wani abu ga gwamnati don kiyaye matsayin kasuwanci ku na doka. |
| Da kyau Don | Kasuwancin iyali • Abokan haɗin gwiwan da suke da dangantaka mai tsawo da juna sannan kuma sun aminta da junan su. | |

# Haɗin Gwiwa Mai Iyaka

A haɗin gwiwa mai iyaka, akwai ma mallaka kala biyu, abokin haɗin gwiwa na gaba daya da kuma abokin haɗin gwiwa mai iyaka. **Abokin haɗin gwiwa na gaba ɗaya** yakan yi aiki kamar yadda mai mallakar kai ka dai yake aiki ko mai haɗin gwiwar gaba ɗaya ta yadda suke gudanar da kasuwancin haɗin gwiwa mai iyaka, yi yarjejeniya, yake shawara da kuma yin aiki a madadin haɗin gwiwa.

**Haɗin gwiwa mai iyaka** shi mai zuba jari ne. Su kan sanya kuɗin su ne kawai sannan su karɓi ribansu amma ba su suke juya harkokin yau da kullum na kasuwancin ba ko kuma yin aiki a madadin haɗin gwiwa. Saɓanin abokan haɗin gwiwa na gaba ɗaya, kadarorin mutum a katange suke ba abun da zai taɓa su. Asarar shi abokin haɗin gwiwa mai iyaka na faɗawa ne kawai akan kuɗin da mutum ya zuba a cikin kasuwancin.

Haɗin gwiwa mai iyaka na buƙatar aiki sosai kafin a fara shi sama da yadda na mallakan Kai ka dai ko haɗin gwiwa gaba ɗaya saboda dole ne ka kai takarda ga Ma'aikatar Jiha ta New York (DOS) kuma ku biya kuɗin haɗin gwiwa. Wannan tsarin kasuwanci yana da kyau ma yan kasuwan da suke da masu saka hannun jari amma basa so su shiga harkokin kasuwancin ko a kansu da alhaki da shawarar da abokan haɗin gwiwa na gaba ɗaya su yanke. Dole ne a rubuta sharuɗɗan ƙayyadaddun haɗin gwiwa mai iyaka a cikin Yarjejeniyar Haɗin gwiwa (duba shafi na 17).

## Sanarwar Jarida

Haɗin Gwiwa Mai Iyaka da Kamfani Lamuni Mai Iyaka ana buƙatar su buga kafa kasuwancin su a cikin jaridu biyu daban-daban har tsawon makonni shida a jere. Wannan ya ta'allaka ne da gundumomi, kuɗaɗen bugawa a jaridun na iya zama da tsada sosai.

### Abokin haɗin gwiwa na gaba daya

- Ya kan zuba kuɗi hannun jarin sa kuma yana karbar rabonsa na ribar
- Ya kan gudanar da kasuwancin da kuma yin shawarwari
- Ya kan yi aiki a madadin haɗin gwiwan.
- Shi ke da alhakin basusukan kasuwancin. (Mai kasuwanci na iya samar da wata hukuma ta daban don zama Abokan haɗin gwiwa na Gaba daya don samar da iyakacin abin alhaki, amma wannan yana kara rikitarwa.)

### Abokin haɗin gwiwa mai iyaka

- Ya kan zuba kuɗi hannun jarin sa kuma ya na karɓar rabonsa na ribar
- Ba ya gudanar da kasuwancin
- Ba zai iya yi aiki ba a madadin haɗin gwiwan
- Kadarorin sa a katange suke. Haɗarin kuɗi yana iyakance ga saka hannun jari na farko.

## Takaitacciyar jawabin Haɗin Gwiwa Mai Iyaka

| | | |
|---|---|---|
| # na masu shi | **masu mallaka 2+** | Akwai ma mallakan kasuwancin kala biyu sannan ana buƙatar akalla daya daga cikin su: abokin haɗin gwiwa na gaba ɗaya da abokin haɗin gwiwa mai iyaka. |
| Farawa | **Yan buƙatan ƙarin koƙari don farawa** | Takarɗun da ake da buƙata don samarwa:<br>▶ Takardun shaidan Haɗin Gwiwa Mai Iyaka<br>▶ Takaddun shaidan Bugawa da Kuma Tabbacin Bugawan (bayan jaridar su buga) |
| Kuɗaɗen/ Takardun | **Yana ɗan tsada** | Dala 200 kuɗin shigarwa, dala 50 kuɗin shigar da Takardar shaidan Bugawa a Jarida, dala 600-1,200 kuɗin yau da kullun na bugawa a jarida. |
| Shirin Haraji | **Sauƙi** | Ku ba da rahoton samun kuɗin kasuwanci a rahoton harajin ku. Hakanan ya kamata a shigar da bayanan haɗin gwiwa. |
| Lamuni | **Mai girma haɗarin kuɗi na kan kin ka ga abokan haɗin gwiwa na gaba ɗaya** | Kowane abokin haɗin gwiwa na gaba ɗaya yana da alhakin bashin kasuwancin sa da kansa. Alhakin abokan haɗin gwiwa mai iyaka ya Kaɗaita ne da iya jarin da suka saka a cikin kasuwancin. |
| Abubuwan da a ke da buƙata masu gudana | **Eeh** | A na buƙatar rubutacciyar yarjejeniyar haɗin gwiwa sannan kuma dole abokan haɗin gwiwa na gaba ɗaya su saka hannun akai. |
| Da kyau don | 'Yan kasuwa wada ke da abokan haɗin gwiwa waɗanda ke son saka hannun jari amma ba sa son shiga cikin yanke shawara ko ɗauka alhaki aiki da kan su. | |

# Kamfani Lamuni Mai Iyaka

Kamfani Lamuni Mai Iyaka (LLC) sukan samar da iyakanceccen abin lamuni ko ƙaramin haɗarin kuɗi na mutum, babbar dama sama da ma mallakar kai ka dai da kuma tsare-tsaren haɗin gwiwa. A ƙarshen doka, shi kasuwancin wani yanki ne na doka daban daga mai (masu kasuwanci) kuma duk masu kasuwancin suna samun kariya ga kadarorin su. Don kiyaye iyakacin abin alhaki, masu mallakar yakamata su buɗe asusun banki daban don LLC, saka ingantaccen jari a cikin LLC saboda su samu daman biyan kuɗaɗen hada-haɗan kasuwancin, ba tare da hada kadarorin su da kadarorin kasuwancin ba sannan kuma kar su yi amfani da kuɗin LLC don hidimar kansu.

Ma mallaka, an sansu akan mambobin LLC ne, za su iya zaɓar gudanar da kasuwancin da kansu ko su wakilta wasu manajoji su ja ragamar kasuwancin. Za a iya ɗaukar manajoji a matsayin ma'aikata kuma a sakamakon haka za a basu izinin yin aiki. **Doka a wannan fanni babu tabbaci, don haka mutanen da basu da izinin aiki za su iya neman shawarar masana doka kafin a ayyana su a matsayin manajan LLC ko da kuwa sune masu mallakan LLC.**

Membobin LLC za su iya zaɓar yadda za a saka harajin LLC lokacin da aka kafa ta. Sai dai idan an yi rajista tare da zaɓen IRS don samun harajin LLC kamar kamfani, mai yiwuwa masu mallakar za su ba da rahoton kuɗin shiga na kasuwanci akan haraji na kan kansu. **Membobin LLC za su iya nemi shawara daga masanin haraji game da zaɓuɓɓukan da suke da su.**

## Yarjejeniyar Aiki

Yarjejeniyar aiki muhimmin takardun ne da LLCs ke amfani da yake ka'idan ce dama, iko, da kuma alhakin mambobin, manajoji, ma'aikata, ko wakilai. Ana iya shigar da Yarjejeniyar Aiki kafin, a lokacin, ko cikin kwanaki 90 bayan shigar da Sharuddan Kungiyar.

## Takaitacciyar jawabin Kamfani Lamuni Mai Iyaka

| | | |
|---|---|---|
| # na masu shi | **Masu Mallaka 1+** | LLCs kan iya samun mamba daya- mai mallaka ko mambobin masu yawa wayanda su ka mallaki LLC. |
| Farawa | **Yana buƙatan ƙarin ƙoƙari don farawa** | Takarɗun da ake da buƙata don samarwa:<br>▶ Sharuddan Kungiyar<br>▶ Takaddun shaidan Bugawa da Kuma Tabbacin Bugawan (bayan jaridar ta buga) |
| Kuɗaɗen/ Takardun | **Tsada** | Dala 200 kuɗin shigar da Sharuddan Kungiya, dala 50 kuɗin shigar da Takardar shaidan Bugawa a Jarida, dala 600-1,200 kuɗin yau da kullun na bugawa a jarida. Ana buƙatar yarjejeniyar aiki. |
| Shirin Haraji | **Matsakaici Rikitarwa** | LLC yana da zaɓuɓɓuka daban-daban dangane da tsarin kasuwanci da kuma adadin mambobi. |
| Lamuni | **Karamin abin alhaki / haɗarin kuɗi** | Kasuwancin wani yanki ne na doka daban daga mai (masu) kasuwancin. Masu mallakan suna da iyakacin alhaki sannan kuma alhakin su ya taƙaita akan iya adaɗin jarin da suka saka a kasuwancin. |
| Abubuwan da a ke da buƙata masu gudana | **Eeh – ajiye bayanai akai-akai** | ▶ Amince da Yarjejeniyar Aiki a cikin kwanaki 90 na cika Takaddun Kungiya.<br>▶ *(Na zaɓi)* A dinga gudanar da tarurruka membobinsa / manajoji<br>▶ Ajiye bayanan LLC da kuma takaddun harajin su<br>▶ Shigar da Bayanin Biennial duk bayan shekaru 2 don tabbatarwa/ sabunta adireshin |
| Da Kyau Don | Masu mallaka wada suke son kiyaye ajiyar kuɗin su da kuma kuɗaɗen su daban daga kasuwancin su kuma suna iya sarrafa abubuwan da ake buƙata. | |


# Kamfani

Akasari ana amfani da kamfani don manyan kasuwanci tare da masu mallaka da yawa saboda yakan ba da damar siyar da hannun jari. Hannun jari yana wakiltar sha'awar mallakan wani ɓangare na kamfani. Kirƙirar kamfani yana buƙatar ɗimbin ayyukan takardu kuma yana da isassun kuɗaɗen gudanarwa da buƙatun doka.

Dole ne kowane kamfani ya kasance yana da dokoki, yan kwamitin gudanarwa, da kuma jami'ai. Bayan an kafa kamfanin, dole ne masu hannun jari su gudanar da taron ƙungiya don kafawa da amincewa da dokoki da kuma zaɓen daraktoci.

Bugu da kari, tsarin Kamfanin yana da matukar hatsari ga yan kasuwa baƙi wadanda ba su da izinin yin aiki. Idan dan kasuwa yana gudanar da kasuwancin a matsayin jami'in kamfani, ko ana biyansa albashi a tsayin ma'aikacin, za a yi la'akari da su ma'aikata ne. Don tabbatar da cewa an kafa kasuwancin ku kuma an gudanar da shi daidai da duk dokokin da suka dace, wanda ya haɗa da dokokin haraji na jiha da tarayya, tabbatar da samun shawarar masanin doka da shawara lokacin haɓaka tsare-tsaren kasuwancin ku. Yadda a ke gudanar da tsarin kamfanoni yana da rikitarwa sannan kuma ya wuce iyakar wannan jagoran.

## Tsarin Kamfani




Wani wanda ya sayi hannun jari a kamfanin kuma ya mallaki kaso na kamfanin bisa yawan hannun jarin da ya mallaka. Bayan an gama kafa kamfanin, akasarin masu mallakan kanfanin sune hannun jari na farko.

Kungiyar mutane da aka zaba don wakiltar ra'ayin masu hannun jari. Daraktoci suma sukan iya kasance masu hannun jari amma ba wai wajibi ba ne. Dole ne hukumar ta kasance tana da mafi karancin darakta ɗaya. Daraktoci su suke da alhakin sa ido a kamfanin, da kuma yanke shawarwarin akan muhimman abubuwan da suka shafi kamfanin.

Su suke da alhakin ayyukan kasuwanci na yau da kullun sannan kuma su na da ikon yin aiki akan ayyukan da suka shafi kasuwanci. **Akan iya daukar jami'ai a matsayin ma'aikata a karkashin doka sannan kuma za a bukaci su tabbatar da matsayinsu na doka don yin aiki a cikin Amurka**

## Taƙaitaccen jawabin Kamfani

| | | |
|---|---|---|
| # na masu shi | **Masu mallaka 1+** | Kamfani akasari suna da ma mallaka masu yawa, wanda aka sani da masu hannun jari, amma za a iya kafa kamfanin da mai hannun jari guda daya. |
| Farawa | **Yana buƙatan ƙarin koƙari don farawa** | Bayan shigar da Takardar shaidan Haɗin kai dole taron kungiya ya gudana don aiwatar da dokokin da ake buƙata kuma a zabi kwamitin daraktoci |
| Kuɗaɗe/ Takardu | **Yana da tsada sosai** | Ana buƙatar Dala 125 dole shigar da Takardun Shaidar Haɗin Kai don a fara gudanar da kamfanin. Kamfani zai iya haifar da kashe makudan kuɗaɗe don doka da/ ko kuɗin bayan akawu. |
| Shirin Haraji | **Yana da rikitarwa sosai** | Ana ƙarfafa gwiwan masu kasuwancin da su tuntuɓi ƙwararren masana haraji don fahimtar wajibcin haraji. |
| Lamuni | **Yana da Karamin abin alhaki / haɗarin kuɗi sosai** | Kasuwancin wani yanki ne na doka daban daga mai (masu) kasuwancin. Masu mallakan suna da iyakacin alhaki sannan kuma alhakin su ya taƙaita akan iya addinn jarin da suka saka a kasuwancin. |
| Abubuwan da a ke da buƙata masu gudana | **Eeh – Sama da tsauraran bukatu masu gudana** | ▶ Taron masu hannun jari na shekara-shekara da na musamman.<br>▶ Toron Kwamitin Daraktoci na yau da kullum da kuma na musamman<br>▶ Adana ajandan taron don kamfanin, takardun haraji<br>▶ Shigar da Bayanin Biennial duk bayan shekaru 2 don tabbatarwa/ sabunta adireshin |
| Da Kyau Don | Manyan kasuwanci tare da masu mallaka da yawa waɗanda ke buƙatar saka hannun jari mai yawa kuma suna son bayarwa da siyar da hannun jari. | |

## Saurin Kwatancen - Wannan tsarin kasuwanci ne yafi dacewa da ku?


| | Mallakar Kai Ka Dai | Haɗin Gwiwa na Gaba Ɗaya | Haɗin kai Mai Iyaka | Kamfani Lamuni Mai Iyaka | Kamfani |
|---|---|---|---|---|---|
| # na masu mallaka | Masu mallaka 1 | Abokan haɗin gwiwa 2+ | Abokan haɗin gwiwa na gaba ɗaya da na haɗin gwiwa mai iyaka 2+ | Mambobin 1+ | Mai (Masu) Saka Hannun Jari |
| Shirye-shiryen Farawa | Sauƙi 🟢 | Sauƙi 🟢 | Matsakaicin Wuya 🟡 | Matsakaicin Wuya 🟠 | Matukar Wuya 🔴 |
| Kuɗi/ Takardun | Babu/ kaɗan 🟢 | Babu/ kaɗan 🟢 | Matsakaicin Mai Tsada 🟡 | Matsakaici Mai Tsada 🔴 | Mai Matukar Tsada 🔴 |
| Shirin Haraji | Sauƙi 🟢 | Matsakaici 🟢 | Matsakaici 🟢 | Matsakaici zuwa m'Mai Rikitarwa 🟠 | Mai Matukar Rikitarwa 🔴 |
| Personal Liability | Sama 🔴 | Sama 🔴 | Sama don Haɗin Gwiwa na Gaba Ɗaya 🔴 | Iyakantance 🟢 | Iyakantance 🟢 |
| Abubuwan da a ke da Bukatu masu gudana | Babu 🟢 | Babu 🟢 | Wasu 🟡 | Wasu 🟠 | Tsada 🔴 |

# Haɗin gwiwar Ma'aikata

Haɗin gwiwar Ma'aikata wani sabon tsari ne na kasuwanci inda ma'aikata suke mallaka da kuma kula da kasuwanci. Ma'aikata yawanci suna ba da gudummawar kuɗi na farko ga ƙungiyar haɗin gwiwa don zama memba sannan kuma a sakamakon haka suna karɓar kason ribar. A wannan tsarin, kowane ma'aikaci yana da damar iri ɗaya da kowa a wajen yin zaɓe a lokacin yanke shawarar da ya danganci kasuwanci kamar su amincewa bada bashi, kwangila da kuma karban bayanin mambobin.

Za a iya samar da Haɗin Gwiwar Ma'aikata ta ɗaya daga cikin tsarin kasuwanci a baya a wannan jagorar wadda ya haɗa da haɗin gwiwa, LLC, ko Kamfani. Yawancin lokaci, haɗin gwiwa ya janyo amfani da tsarin LLC ne saboda sauƙin sa da kuma yana buƙatar kuɗi kadan don kafawa da kulawa da kasuwancin fiye da kamfani sannan kuma shine yafi dacewa wajen masu mallakan kasuwancin dayawa sama da haɗin gwiwa. Haɗin gwiwar LLC yana ba da iyakacin abin alhaki ga membobi. Haɗin gwiwar zai taimaka wajen kare baƙi marasa shaidan doka daga ana amfani da su ta hanyar satar albashin su ko cin zarafi su.

Jihar New York tana da Dokar Kamfanin Haɗin gwiwar Ma'aikata na musamman da aka haɓaka da kuma ƙa'idodin da suka danganci zama memba, hannun jari da rarraba riba da kuma asara. Don ƙarin bayani, Dan Allah ku ziyarar ci shashin albarkatu na wannan jagoran.



# Ma'anoni

### Shaidawa
Bayanin rubuce-rubuce da sa hannu da aka tabbatar da wanda aka ba shi izini a ƙarƙashin doka, kamar notary.

### Kwamitin Daraktoci
Kungiyar mutane da aka zaɓa don wakiltar ra'ayin masu hannun jari a cikin kamfani da kuma ba da kulawa da kasuwanci gaba ɗaya da kuma yanke shawara.

### Abokin hulɗan
Mutum ne ko kasuwanci da ya ke karɓar aiki daga ɗan kwangila mai zaman kansa.

### Dan kasuwa
Mutum ne wanda ya shirya kuma ya ke gudanar da kasuwanci shi.

### Wanda ke ɗaukar aiki
Mutum ne ko kasuwanci da ya ke da alhakin biyan albashi da kuma ɗaukar wani mutum a aiki.

### Lambar Shaida ta Mai Biyan Haraji (ITIN)
Lamba ne wanda Cibiyar Harajin Cikin Gida ta ke bayarwa ga mutane da basu cancanci a basu lambar Tsaro amma wadanda suna da buƙatar biyan haraji.

### Cibiyar Haraji Na Cikin Gida (IRS)
Cibiyar gwamnatin tarayya ne wanda ke da alhakin karɓan harajin tarayya.

### Lamuni
Wani adadin doka ne ko alhakin kuɗi ko haɗarin da ke da alaƙa da kasuwanci.

### Memba
A wajen Kamfanin Lamuni Mai Iyaka masu mallakan kasuwancin ana dangantasu da membobi.

### Jami'ai
Jami'ai sune masu kulawa da hada-haɗan yau da kullum na kamfani. Wanda Kwamitin Daraktoci ya zaba, jami'ai za su iya zama su ne suka kirkiri/ masu mallakan kamfanin da kuma wasu adadin ma'aikatan kamfanin.

### Haɗin Gwiwa
Wani tsarin kasuwanci ne wanda mutane biyu ko fiye da haka su ka mallaki kasuwancin. A haɗin gwiwa na gaba ɗaya, abokan haɗin gwiwa sukan raba alhakin da riba ko asaran kasuwancin. A haɗin gwiwa mai iyaka, wasu abokan haɗin gwiwa su ke gudanar da kasuwancin sannan wasu daga cikin abokan haɗin gwiwa sukan saka hannun jarin ne a cikin kasuwancin kaɗai amma dukan abokan haɗin gwiwa sune masu kasuwancin.

### Mai Mallaka
Shine mai kasuwancin

### Masu saka hannun jari
Masu saka hannun jari wasu mutane wadanda suke siyan hannun jarin kamfani. Masu sa hannun jari sune suka mallaki wani yake na kuɗin da suka saka a kamfani.

# Takardun Masu Muhimmanci

### Sharuddan Kungiyar
Takardun da ke zayyana sunayen kamfani Lamuni Mai Iyaka (LLC), gundumar da adireshin da ake buƙata wajen ƙirƙirar LLC. A na ƙirƙirar LLC ɗin ne lokacin shigar da Sharuddan Kungiyar ko wani lokaci daga baya wanda aka fayyace a Sharuddan Kungiyar, kar dai ya wuce kwanaki 60 daga shigarwan.
*An shigar da shi ga Ma'aikatar Jiha*
▶ Kamfani Lamuni Mai Iyaka

### Bayanin Biennial
Ana buƙatar duk bayan shekaru biyu NYS LLCs da Kamfanonin su shigar da Bayanin Biennial sannan kuma ku biya kuɗin shigarwan dala 9 don tabbatarwa ko sabunta adireshin kasuwancin.
*An shigar da shi ga Ma'aikatar Jiha*
▶ Kamfani Lamuni Mai Iyaka ▶ Kamfani

### Dokoki
Rubuttacen takardan da ya bayyana yadda kamfani zai gudanar da ayyukan sa. Wannan bayanan sun haɗa da yadda za a zabi Daraktoci, yadda za a gudanar da taro, da kuma menene hakkoki, ayyuka da ikon masu hannun jari, daraktoci da jami'ai.
*Dole a ajiye kwafi daya a kamfanin.*
▶ Kamfani

### Takardan Shaidar Saka Suna
Takarda kawai a ke buƙata lokacin da sunan kasuwancin ya sha bambam da sunan ma mallakin kasuwancin.
*An shigar dashi ga magatakardar gundumar*
▶ Mai Mallakar kai ka dai ▶ Haɗin Gwiwa na Gaba Ɗaya
▶ Duk wani kasuwancin da ke aiki karkashin wani suna daban daga sunada na doka

### Takardun Shaidar Haɗin Kai
Takarda ne da ya wanda ya fayyace suna da adireshin kamfani. Kafuwar Kamfani na farawa a ranar da aka shigar da Takardar shaidan Haɗin kai ko a wani lokaci na gaba ( tsakanin kwanaki 90 daga ranar da aka shigar) wannan da aka fayyace a cikin takardan shaidn haɗin kan.
▶ Kamfani

### Takardun Shaidar Haɗin Gwiwa Mai Iyaka
Takarda ne da ya shimfida sunaye da kuma bayanan abokan haɗin gwiwa da suka shiga cikin yarjejeniyar haɗin gwiwa mai iyaka.
*An shigar da shi ga Ma'aikatar Jiha*
▶ Haɗin Gwiwa Mai Iyaka

### Takardan Shaidar wallafa
Takarda ne da kuka aika da takardan rantsuwa wa jaha don tabbatar da cewa kun yi biyayya ga sharruɗonɗin wallafa kasuwancin ku a jarida don fara haɗin gwiwa mai iyaka ko LLC ( duba shafi na 19 da 22). Dole a shigar da Takardar Shaidan Wallafa a tsakanin kwanaki 120 bayan an shigar da Takardar shaidan Haɗin Kai Mai Iyaka ko Sharrudan Kungiya.
*An shigar da shi ga Ma'aikatar Jiha*
▶ Haɗin Gwiwa Mai Iyaka
▶ Kamfani Lamuni Mai Iyaka

### I-9 Takardan Bincika Tabbacin Cancantan Aiki
Takarda ne da zai tabbatar da duk ma'aikata do ka ta amince da su yi aiki a Amurka. Mai gidan ku dole ya karbi takardan I-9 sannan kuma ya bada shi ga jami'an gwamnati Amurka don bincike.

### Yarjejeniyar Aiki
Akan ƙayyade haƙƙoƙi, iko, abubuwan da ake so, iyakoki ko alhakin membobi, manajoji, ma'aikata ko wakilai. Ana iya shigar da Yarjejeniyar Aiki kafin ko cikin kwanaki 90 bayan shigar da Sharuddan Kungiya.
*Dole a ajiye kwafi daya a LLC*
▶ Kamfani Lamuni Mai Iyaka

### Yarjejeniyar haɗin gwiwa
An ba da shawarar ga haɗin gwiwa na gaba ɗaya kuma ana buƙata don haɗin gwiwa mai iyaka, yana kafawa da tabbatar da tsare-tsare, hakkoki da wajibai a tsakanin abokan haɗin gwiwar kasuwanci.
▶ Haɗin Gwiwa Na Gaba Ɗaya ▶ Haɗin Gwiwa Mai Iyaka

# Albarkatu

## Cibiyar Gwamnatin Jahar NY

### Ma'aikatar Jiha, Sashen Kamfanoni, Bayanan Jiha, da UCC

www.dos.ny.gov/corps/

Bayani akan da samfura na takardu da sauran takaddun doka waɗan da Wataƙila za a buƙata don buɗewa ko faɗaɗa kasuwanci a Jihar New York.

### Cigaban Jahar Empire, Shirin Taimakon Kasuwanci

esd.ny.gov/entrepreneurial-assistance-program

Shirin Taimakon Kasuwanci (EAP) an ƙirƙiri cibiyoyin EAP a cikin al'ummomin gida a ko'ina a cikin Jihar New York don ba da umarni, horarwa, taimako, da kuma ayyukan taimako ga daidaikun mutane wadan da suka fara kasuwancin su kwanan nan ko wadan da su ke sha'awar fara kasuwanci.

### Ofishin Sabin Amurkawa (ONA)

1-800-566-7636

www.newamericans.ny.gov/business

Ofishin Sabbin Amurkawa yana da cibiyoyin dama guda 27 a duk faɗin jihar New York don samar wa baƙi bayanan ilimi da albarkatun tattalin arziki wada suka haɗa da taimakon ƙananun kasuwanci.

### Cibiyar haɓaka ƙananun kasuwanci (SBDC)

1-800-732-7232

www.nysbdc.org/

Ta hanyar cibiyoyin yanki 24, Cibiyar haɓaka ƙananun kasuwancin jahar New York (NYS SBDC) suna bayar da mafi ingancin, shawarwarin da horarwar kasuwanci a kyautata ko a farashin mai sauƙi yan New York masu sha'awar fara kasuwanci ko inganta harkokin kasuwancin su.

## Cibiyoyin Gwamnatin NYC

### Sashen Harkokin Masu Amfani, Ofishin masu ƙarfafa gwiwa na Kuɗi

www.nyc.gov/site/dca/partners/financial-empowerment.page

Ilimin harkokin kuɗi da ba da shawara da aka samar da su da nufin ƙarfafawa da kariya ga ƙananan masu kuɗin shiga yan New York waɗanda ke son haɓaka kadarorinsu da kuma su yi amfani da mafi yawan albarkatun kuɗaɗen su. Sun haɗa da bayani akan mafi tsaro da kuma sauƙin hulɗan da babban banki da kuma samun damar samun kuɗaɗen haraji na haɓaka kuɗin shiga.

### Ayyukan Kananun Kasuwanci (SBS)

https://www1.nyc.gov/nycbusiness/

Darrusa kyauta, tarurukan bita, shawarwari da kuma taimakawa yan kasuwa masu buƙatan su ƙirƙiri, aikin, ko haɓaka kasuwancin su a Birnin New York.

### SBS na Kaddamar da Kasuwancin Baƙi

www1.nyc.gov/nycbusiness/article/immigrant-business-initiative

SBS suna kiyaye da darussan kasuwancin, taimakon kudi, ayyukan shari'a na pro-bono, da kuma yarurruka masu yawa a gaba ɗaya Birnin New York ba tare da ko sisi ba.

## Kungiyoyin NYC:

### Laburaren jama'a na Brooklyn, Kananun Kasuwanci da kuma Ayyukan Kasuwanci

www.bklynlibrary.org/business/small-business

Wurare daban-daban a ko'ina a cikin Brooklyn, tarurukan bita, azuzuwa, da kuma keɓantacen taimako a harshen turanci, sifen, Rashanci, da Kreyol akan fatawa, gudanarwa, da kuma haɓaka kasuwanci.

### Cibiyar Isar Da Sakon Kasuwanci (BOCNET)

www.bocnet.org

Kananan kamfanoni, ƙananan ƙungiyoyin ci gaban kasuwanci wanda suke samar da ayyukan kasuwancin na musamman a cikin Bronx, Brooklyn, Manhattan, Queens, Staten Island ga al'ummomin da ba a ba su ba, ciki har da ƙananan lamuni na kasuwanci, kula da yara na gida, tarurrukan 'Business American-Style', da 'yan gudun hijira Micro-Interprise Project.

### Ayyukan kananun kasuwanci na CAMBA

718-287-2600

www.camba.org

Keɓantatton shawarwari, taron bita na kananun kasuwanci, shawarwarin kasuwanci, haɗa ku da wasu abokan haɗin gwiwa cigaban kananun kasuwanci, da kuma bashin kasuwanci.

### Ayyukan Ci gaban Al'umma, Kungiyar Taimakon Shari'a

212-426-3000

www.legalaidnyc.org/civil-practice-pro-bono-projects

Ana gudanar da horo ga masu ba da shawara da

# Albarkatu

kuma jama'an da abokin ciniki da suka cancanta a gaba ɗaya gundumomi 5. Batutuwa sun haɗa da fara Kananun kasuwanci, sanya hannu kan yarjejeniyar kasuwanci, kare kasuwanci da kuma kadarori. Ana yin horo a cikin harcen Turanci da kuma sifen.

### Cibiyar Koyar da Ilimin Birane (CUP)
www.welcometocup.org
Buga ƙasidu da litattafai don demystify rikitattun manufofi da matakai, wanda ya haɗa da Jagora ga Co-Ops na Ma'aikata a NYC.

### Kungiyar Lamuni kyauta na Hebrew
www.hfls.org/loan-programs/microenterprise/
Ba da bashin Kananun yan kasuwa wanda babu kuɗin ruwa a ciki ga mazaunan birnin New York, Long Island, da kuma Westchester masu karami da matsakaicin karfi, don su fara ko haɓaka kasuwancin su.

### Aikin Dokokin Kasuwa na Maƙwabta, Cibiyar Shari'a ta NYC Bar
212-382-6633 (ainihi)
212-626-7383 (layin karta kwana na doka kyauta)
nelp@nycbar.org
Ayyukan shari'a don ƙananan yan kasuwa masu karamin da matsakaici ƙarfi don fara kasuwanci, gami da batutuwan haraji, kwangiloli da yarjejeniyoyin, cinikayya haya na kasuwanci, haƙƙin mallaka, alamun kasuwanci, da haƙƙin mallaka fasaha.

### Kamfanin Raya Tattalin Arziki na Renaissance
www.renaissance-ny.org
Cibiyar Ci gaban harkan kuɗaɗen na Al'umma wanda suka mai da hankali a kan canza baƙi, da al'umma masu ƙanana da matsakaitan ƙarfi a cikin NYC ta hanyar samar musu da bashi mai sauƙi kuɗin ruwa da kuma shirye-shiryen horar da yan kasuwa.

### Masu Sa-kai na Ayyukan Shari'a
347-521-5729
www.volsprobono.org/projects/microenterprise-project
Sukan taimaki masu Kananun kasuwanci da Kananun yan kasuwa wajen samu kyakkyawar, ayyukan doka kyauta daga jajurtatun ma'aikatan da kuma toron lauyoyin pro bono.

## Albarkatun Haɗin gwiwar NYC:

### Ma'aikatan Green Coop
www.greenworker.coop
Suna ba da ingantaccen horo na tsawon watanni 5 da kuma shirin tallafi wanda ke taimakawa ƙungiyoyin yan kasuwa masu burin haɓaka kasuwancin kore na ma'aikata kuma suna amfani da haɗin kai na horo, koyawa, da ayyukan fasaha.

### Cibiyar haɗin kan Ma'aikata na birnin New York (NYC NOWC)
212-390-8178 (Layin karta kwana)
www.nycworker.coop
Ci gaban jagoranci, horarwar, taron bita, taimakon kasuwanci, da kuma taimakon ta hanyar fasaha a kan haɗin gwiwar ma'aikata da kuma ƙwarewar kasuwanci na haɗin gwiwa.

### Workers Justice Project - Make The Road New York
347-889-6347
www.workersjustice.org
Kungiyar yanci baƙi da sauran batutuwa suna aiki ne don samar da ayyukan yi masu dorewa ta hanyar ƙungiyar, tallafi da haɓakaw ƙungiyoyin haɗin gwiwar ma'aikata.

## Kayayyakin Yanar Gizo:

### New York Business Express
www.businessexpress.ny.gov
Yana taimakawa wajen jagoran tar ku akan kasuwanci ku da buƙatun kwararru. Ku na cika takardun tambayoyin Business Wizard zai samar muku da jerin duk abin da kuke buƙata don fara kasuwancin ku.

### NYC Business Portal
www1.nyc.gov/nycbusiness

**Mataki-matakin Takardun Tambayoyi**
Cika takardun tambaya mataki-mataki sai ku samu jerin lasisi na musamman na birni, jihohi da kuma tarayya da izini da za ku buƙaci farawa da sarrafa kasuwancin ku bisa masana'antar da kuke aiki a ciki.

**Kimanta Karfafa gwiwa**
Cika takardun tambayoyi ku samu jerin abubuwan ƙarfafa gwiwa na gwamnati da kuɗaɗen harajin da gwamnati za ta yafe muku da kasuwancin ku kan iya cancanta.